# Cewa Talbiyar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -: "AmsawarKa ya Allah, amsawarKa, amsawarKa baKa da abokin tarayya amsawarKa, lallai cewa godiya da ni'ima na Ka ne kuma mulki ma naKa ne, baKa da abokin tarayya

Daga Abdullahi ɗan Umar - Allah Ya yarda da su -: Cewa Talbiyar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -: "AmsawarKa ya Allah, amsawarKa, amsawarKa baKa da abokin tarayya amsawarKa, lallai cewa godiya da ni'ima na Ka ne kuma mulki ma naKa ne, baKa da abokin tarayya" Ya ce: Abdullahi ɗan Umar - Allah Ya yarda da su - ya kasance yana ƙarawa a cikinta: AmsawarKa amsawarKa, da taimakonKa (akan aiki), alheri yana hannayenKa, amsawarKa fata yana gareKa da kuma aiki.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Talbiyyar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ta kasance idan ya yi nufin shiga aikin Hajji ko Umarah ita ce ya ce: (AmsawarKa ya Allah amsawarKa) amsawa ta lazimi gareKa bayan amsawa a cikin abinda Ka kiramu na ikhlasi da tauhidi da hajji da wasunsu, (AmsawarKa baKa da abokin tarayya amsawarKa) Kaine Kai kaɗai wanda ka cancanci a bauta maka, baKa da abokin tarayya a rububiyyarKa da UluhiyyarKa da sunayenKa da siffofinKa, (lallai cewa godiya) da godiya da yabo (da ni'ima) daga gareKa Kaine Mai bada su (gareKa ne) ana juya su a kowane hali, (mulki ma) kamar haka naKa ne, (baKa da abokin tarayya) dukkansu naKa ne Kai kaɗai. Ibnu Umar - Allah Ya yarda da su - ya kasance yana ƙarawa a cikinta: (AmsawarKa amsawarKa da taimakonKa) Ka taimakeni taimako bayan taimako, (alheri yana hannayenKa) dukkansa kuma daga falalarKa ne, (amsawarKa fata gareKa ne) da nema da tambaya zuwa wanda alheri yake a hannunSa, (aiki ma) gareKa ne Kaine wanda ya cancanci a bauta masa.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee